# IN AN GIRMA A SAN AN GIRMA

Mounkaila Hamadou Gandozi
Niamey, Niger
2002

Sofo
Yaya a ke haka
Kurciya a gare ka
Jiya ne,ba yaw ba
Yaw ka girma
Tahiyan dare,biyan lunguna
Ba naka ba
Zama a kan titi
Ba naka ba

Lattijo ka yi tunani
Way gaka a fada
Jabba ta sha kura
Wata,yarin ya ce
Ko macen aure ce
Ta fice,ka kalle ta
Wani ya fice,a cikin shaanin sa
Way ma ya gayda ka
Amma sai ka bace shi

"Wai,wagga dia wacece?
Amma curciyagga ta iya batanci!
Wai wannan samari da ya wice
Kun san da uban shi bayada ko sisi
Ku ga tahiya shi kaman sarci"
kallamomin da ka iyaan nan

Lattijo ka yi tunani
Ina ka baro ya yanka
A she ma ka baro guida
Ba abinci balle kayan miya
Sai dai gulma da kormoto

Sofo gara dai ka dena
Ka iya zama guida
Ko yara da jikoki
Su samu tarbiyan korey
Zama a masallaci da jan tabzi
Su a naka
Ya kamata lattijo
Ka zama hascen fitilar mu
Kal duhun dunia shi rife mu
Kal mu dau hanya na batawa

Sofo yaya a ke haka
Ka san da kai makiayi ne
Gara ka dau sandar ka ta adalci
Mu samu ima halaka
Ka san da kai manomi ne
Ka iya kula da gonar ka
Kal gniwar imani ya share mu

Kaka ko baba ne
Ko ma yayan mu ne
Lattijo a yi tunani
In an girma
A san an girma